**EPISODE 1**

<u>**CHARACTERS**</u>

*LARABA*

*HANNAH*

*HUSSEINI*

*ASABE*

*LANTANA*

**SCENE 1**

**ZARIA. PERI-URBAN AREA, LANTANA'S HOME.**

| | | |
|---|---|---|
| 1. | **MUSIC:** | <u>**THEME MUSIC**</u> |
| 2. | **SFX:** | <u>**MUSIC PLAYING LARABA AND HANNAH LAUGHING.**</u> |
| 3. | **HANNAH:** | **(EXCITEDLY)** Yauwa Laraba!,yanzu ni ke da ke! |
| 4. | **LARABA:** | **(LAUGHING SHYLY)** Hannah, me kike nufi? A cikin dukan jama'a kin san ai cewa ina nan ko da yaushe domin ki . |
| 5. | **HANNAH:** | Ah, tun da aka suma shirin auren ki, ban sa ki a ido na ba, kullun kina tare da wanchar kauwar ko kuma wata kawar. |
| 6. | **LARABA:** | **(TEASING)** Haba Hannah, ko kina kishi ne? kin san dai ai duk locacin da kike bukata ta ai ina nan domin ki |
| 7. | **BOTH:** | **(LAUGH)** |

8. **HANNAH:** **(STILL LAUGHING)** Ai na sani. **(SERIOUS)** Maganan gaskiya, kwana biyu kuma ina yi miki murna

*9.* **LARABA:** **(NERVOUSLY)** Hannah, Ina fatan komai zai tafi daidai,.

*10.* **HANNAH:** Ki kwantar da hankalin ki, me kike jin zai bada matsalla? Jallon na mutukar sonki kwarai, za ku same zaman lafiya.

*11.* **LARABA:** **(RELIEVED)** Oh Hannah! Ke kawata ce na gaske, kamar yanzun da ki ka bar mai gidan ki shi kadai – ki zo ki taya ne hira.

*12.* **HANNAH:** hakika! Laraba, ke aminita ce ai, ki dai bar zancen, dubi yadda ki ke killi, Jallon a da sa'a

13. **LARABA:** **(SERIOUSLY)** Hannah, amma ni da ke mun san – nine da sa'a, duk jama'a suna ganin Jallo yayi rashin hankali sha'awar aure na saboda bakin jinni da ke tare da ni

14. **HANNAH:** Laraba, kul! Babu wani abu wai rasher sa'a! ba laifin ki bani ai cewa ki kadai ke ka rayu a hadarin gobaran wutar da ta hanlaka iyayen ki da sauran yanuwan ki ai.

15. **LARABA:** (**DRY LAUGH)** kwarai! Jama'a kalilan ne suke da irin ra'ayin ki.

16. **HANNAH:** Madallah, Jallon yana cikin wadanda ke da irin ra'ayin, shine kuma abinda yafi muhimmanci

17. **LARABA:** **(HAPPY)** Kina da gaskiya Hannah, Jallo bait aba damuwa da kalamai marasa dadi da jama'a key i game da ne ba ko kuma rashin sa'ar ba.

18. **HANNAH:** **(TEASING)** Laraba, idan ke ka ci gaba da fadin wai rasher sa'ar ki, zan gaya ma aunty Lantana fa. Jallo ba sakari ne ba ai, ba zai so ya rasa kyakyawa kamar ke wai saboda da gulmar jama'a ba ai.

19. **LARABA:** **(LAUGHING)** Hannah! **(SERIOUS)** ko ki san cewa dangin Jallo sun aminci da ni sosai? Tun daga mahaifiyarsa zuwa yan'uwan sa mata har da saurar mata da ke dangin sa

20. **HANNAH:** Ba abin mamaki baba ne ai!

21. **SFX:** <u>**DRAWER OPENS AND CLOSES**</u>

22. **LARABA:** Hannah, dubi sarka da gyallen amarchi da kishiyar mahaifiyata ta sayamin

23. **HANNAH:** **(EXCITEDLY)** wai! Sun yi kyau kwarai! Na yarda da aunty Lantana ai, tana da kirki da tunani ai, gobe zaki fito tamkar gimbiya.

24. **LARABA:** Hajiya Lantana, kishiyar mahaifiyata abar alfahari ne a rayuwata, it ace ta dauke ne da bala'I ta auko min na rashin iyaye na da yan'uwa na, duk da cewa sun rabo da mahaifina a lokacin.

25. **HANNAH:** Hajiya Lantana, bata ganin ki kamar ba wace ta Haifa ba, ta dauke ki tamkar wanda ta Haifa, tana kaunar ke sosai kuma tana alfahari da ke .

26. **LARABA:** Ah Hannah, ina kaunar ta ni ma, kuma ina fatan zan zama mata sanadin albarka a rayuwar ta.

27. **HANNAH:** Ni dai ba zan iya jiran sai ranar aure in ga kyau ki ba, don Allah ki sa sarkokin domin in gani.

28. **LARABA:** (**LAUGHING)** Toh Hannah, amma domin ke che fa. **(PAUSES)** Toh ki zo ki hada min mahadin sarkar. **(PAUSES)** Toh ga shi na sanya, yaya ki ka gani.

29. **HANNAH:** Hmmm, Laraba kin yi kyau kwarai, Jallo yayi sa'armata.

30. **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**SCENE 2**

**NORTHERN KADUNA. HAJIYA INNA'S HOUSE. HUSSEINI AND ASABE'S BEDROOM. EVENING.**

31. **SFX:** **<u>SOUND OF DOOR OPENING AND CLOSING</u>**

32. **HUSSEINI:** **(SLIGHTLY BREATHLESS)** Ah, Asabe ki che anan, na dubi yaran har sun yi barci

33. **ASABE:** **(COLDLY)** E Hussaini, sun yi barci.

34. **HUSSEINI:** **(DISAPPOINTED)** Ayyah, ta taho musu da alawa. **(PAUSES)** Toh, sai a basu gobe kawai

35. **ASABE:** **(COLDLY)** Ba matsala zan basu gobe

36. **SFX:** **<u>SOUND OF BED CREAKING AS HUSSEINI SITS</u>**

37. **HUSSEINI:** **(CONCERNED)** Me ke damun ki Asabe, kamar ranki a baci game da wani abu.

38. **ASABE:** (**STILL COLD)** Hmm Mai gida, ba abin da ya bata min rai.

39. **HUSSEINI:** Asabe, kin san na san halayin ki kwarai, zan iya gani wa indan kina fushi.

40. **ASABE:** Toh, indan ka dage – kana son sani, kayi min alkawarin cewa zaka bani wasu kudi tun wancin makon amma har yanzu ba labari.

41. **HUSSIENI:** **(UPSET)** Asabe, yaya kike yi kamar baki san halin da muke ciki ba, ki kudi kawai kike sa a zuciyar ki?!

42. **ASABE:** Amma ne ci matar gidar ai Husseini, dole in ya kudi a zuciya ta, nice ki sa ma yaran tsofofin tufafi ai

43. **HUSSEINI:** **(CUTS IN, UPSET)** Kina tsamani inna jin dadi dogara a kan danuwana Hassan ne, a matsayi na namiji?

44. **ASABE:** **(APOLOGETIC)** Na san baka jin dadin haka, sai ya sa nake maka adu'a. Allah bada sa'a kullum.

45. **HUSSEINI:** Toh me ya sa keki matsamin akan batun kudi bayan kin san kusan shekara kokari nake in tara jari.

46. **ASABE:** (**REMORSEFUL)** Allah ya huchi zuciyan ka maigida na, na matsa maka ne akan kayan yaran saboda kayi mana alkawari.

47. **HUSSEINI:** Ke ma Allah baki hakuri, na san bana iya samar muku abin da suka kamata sanadiyar rasa aiki na da nayi a Abuja.

48. **ASABE:** Ba komai maigida na, komai zai wuce abu mafi muhimmunci shine muna ra'ayi

49. **HUSSEINI:** **(FRUSTRATED)** Asabe, inna ki ke ganin zan same jarin in fara kasuwancin saida shayi da muka tautaunawa.

50. **ASABE:** Maigida na dole ne ka kokarta!, na tabbata akwai wanda zai iya taimaka ma, meya sa baza ka tabbayi

Hassan ba? Yayi fiche a cikin kungiyan su ta yan kasuwa, na tabbata ya san mutane!

51. **HUSSEINI:** (**RELUCTANTLY)** Hassan ya kokarta mana fa Asabe. Bana sun in takura masa da wannan matsalar, kuma shi ma abubuwan ba kamar da ba ne.

52. **ASABE:** Ba kamar da ba? Ai naga dashi da Jummai suna iya biyan bukatun su cikin sauki.

53. **HUSSEINI:** Asabe, ki tuna fa sun riga mu fara tazaran haihuwa, suna da ajiya da saurar su. Mu ko bamu dadie da farawa ba, zai dan dau lokaci ai.

54. **ASABE:** (**UNIMPRESSED)** duk da haka, na san zai iya taimaka maka, kuma ai ba kudi kake bukata a wurin sa baa i, illa a had aka da jama'ar da za su taimaka maka.

55. **HUSSEINI:** Asabe, ki kara yin hakuri, kin ji? Ina samun kudi zan baki kudin da ke ki bukatar. **(TEASING)** Harma fiye da haka, kin ji?

56. **ASABE:** **(HAPPY)** Toh Husseini, na yarda da kai, amma duk Allah kada ka bar ni in ta jira, ya kamata mu fara sayyayen golagolen auren Raliya da sauri. Wata kauwata ta kawo…

57. **HUSSEINI:** **(CUTS IN, AMUSED)** Kul Asabe! Raliya har yanzu karamar yariya ce. Kada ki damu, da iznin Allah komai zai yi mana daidai ba da jimawa ba.

58. **ASABE:** Fata na kenan, Maigida na. baza mu iya ci gaba haka ba.

59. **MUSIC:** <u>**BRIDGE MUSIC.**</u>

**SCENE 3**

**ZARIA, LANTANA'S HOME. EARLY AFTERNOON.**

| | | |
|---|---|---|
| 60. | **SFX:** | **<u>MUSIC PLAYING. DOOR OPENS AND CLOSES.</u>** |
| 61. | **LANTANA:** | Yauwa Laraba, amshi ya ta. |
| *62.* | **LARABA:** | **(SURPRISED)** Kai! Karin sarkoki da kaya? Amma, Hajiya Lantana ai kin riga kin bani sarkoki ai. |
| *63.* | **LANTANA:** | ba abin da zan baki da zai yi yauwa yata, kefa abin alfaharita ce, ina son ki zama cikin murna sosai kuma kada ki rasa komai a wannar babbar ranar na ki. |
| *64.* | **LARABA:** | **(ACCEPTING THE GIFTS)** Nagode Kwarai, Hajiya Lantana, Allah saka me ki da alheri. |
| *65.* | **LANTANA:** | Ni ke da godiya Laraba,**(PAUSES)** Dubi yadda ki ka yi kyau! Kyau da ilimi. Ina alfahari da ke |
| *66.* | **LARABA:** | (**VOICE CHOKED WITH EMOTION)** Na gode mama, nagode da dukan taimako da kaunar da ki ka nuna min duk da dukan jama'a suka juya min baya **(WEEPING).** |
| *67.* | **LANTANA:** | Me haka Laraba? Hawaye? Ranar auren ki? Yata, ki daina, murna yakamata ki yi. toh yin min murmushi. |
| *68.* | **LARABA:** | (**SMILING)** Hawayen murna ne mama, ina cike da farin ciki. |
| *69.* | **LANTANA:** | Murna ya chanchanta ki yi, Jallo mutumin kirki ne ai, kuma yana mutukar son ki. |
| *70.* | **LARABA:** | Ai, Hajiya ina ciki da farin ciki, na gode. |
| *71.* | **LANTANA:** | Haba Laraba, ba sai kin dinga yi min godiya ba ai, ina farin ciki abubuwa suna tafiya miki yadda ya kamata. |

**SCENE 4**

**ZARIA, PERI-URBAN AREA, LANTANA'S HOME.**

72. **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

73. **SFX:** **<u>JUBILATION AND MERRY MAKING ALL ROUND. SOUND OF ULULATIONS. CHATTING AND LAUGHING ALL OFF MIC. ON MIC LOW MUSIC PLAYING IN A ROOM.</u>**

74. **HANNAH:** Hakika, Laraba kin yi kyau mutuka, tabas Jallo zai rudei in ya gan ki,

75. **LARABA:** (**WORRYING)** Hmmm Hannah, na soma damuwa fa, ya kamata a ce shi da jama'ar sa sun iso yanzu, na tabbata jama'a sun soma maganganu.

76. **HANNAH:** Labara, kin fiye damuwa. Ba'a zargin komai **(TEASING)** Suna nan suna ta cin kayan dadi, ba kamar ke ba.

77. **LARABA:** **(DISTRESSED)** Tayaya zan iya cin wani abu, Hannah? Na san Jallo, ba ya son makara. Gaskiya na damu.

78. **HANNAH:** Labara, ba wai ya makara sosai ba ai, kilar suna cikin goslow ko kuma motar ta sami matsalla.

79. **LARABA:** (**REALLY WORRIED)** Mutumin bat un asali baya makara, sai a ranar dauren aurensa, abin da mamaki. Ni dai na damu.

80. **HANNAH:** Kilan yan'uwan sa sun tsaba makarewa, kin san dole ne ya jira su ai.

| | | |
|---|---|---|
| 81. | **LARABA:** | ina fatan haka fa, Hannah. Na fara jin kamar wani abun na faruwa, ina kirar wayar shi Jallo amma baya ya dauka. |
| 82. | **HANNAH:** | Labara, kin fiye damuwa, ki kwatar da hankalin ki |
| 83. | **LARABA:** | Toh Hannah, Zan kokarta…... |
| 84. | SFX: | **COMMOTION OUTSIDE. SOME WAILS. CONFUSION.** |
| 85. | **LARABA:** | **(WORRIED)** Hannah, me haka? Me yasa jama'a ke ihu a waje? |
| 86. | **HANNAH:** | Labara, kwantar da hankalin ki, bara in je in duba… |
| 87. | **SFX:** | **SOUND OF DOOR BEING OPENED HURRIEDLY AND SLAMMING SHUT** |
| 88. | **LANTANA:** | **(BURSTING IN WEEPING)** waiyo, yata! Laraba taa..! |
| 89. | **HANNAH:** | Ah, Meya ke faruwa Hajiya Lantana?! Ki fada mana, don Allah! |
| 90. | **LARABA:** | (**LOSING CONTROL)** Hajiya! Mama! Ki yi Magana, don Allah me ya faru?! Hajiya! |
| 91. | **LANTANA:** | **(WEEPING )** Laraba, Jallo da yan uwansa sun yi hatsarin mota akan hayar sun a zuwa nan, kuma…… (**MORE WEEPING)**.. |
| 92. | **HANNAH:** | Don Allah, Hajiya, ki daure ki fada mana. Mu ma'aikatan lafiya ne, ina suke? Kilar zamu iya taimaka wurin kulla da su. |
| 93. | **LANTANA:** | **(WAILING)** Jallo ya rasu! Shi da yan'uwansa! Wata babbar mot ace ta kwaci ta buge su akan hanyarsu na zuwa nan. |

94. **LARABA:** (**WAILING AND WEEPING)** Waiyoooo!!Me yasa haka ke faruwa da ni?

95. **SFX:** **<u>SOUND OF CHAIR SCRAPING THE FLOOR AS LARABATHROWS HERSELF TO THE GROUND</u>**

96. **HANNAH:** **(COMFORTING)** Kai Laraba, ki daure, za ki yi ma kanke rauni fa.

97. **LANTANA:** **(SADLY)** Yata abinda ya faru kadara ne daga Ubangiji, kinji? Kiyi hakuri, komai zai daidaita.

98. **LARABA:** Ba abinda zai daidaita, bakin jinina ya ja min.

99. **MUSIC:** **<u>THEME MUSIC</u>**